Cewa Manzon Allah SAw ya kasance ian ya yayi Ruku'u yana rarraba 'Yanyatsunsa kuma idan yayi Sujada sai ya haxe su

Daga Wa'il Bn Hajar -Allah ya yarda da shi- Cewa Manzon Allah SAw ya kasance ian ya yayi Ruku'u yana rarraba 'Yanyatsunsa kuma idan yayi Sujada sai ya haxe su
[Ingantacce ne] [Ibnu Hibban ne ya Rawaito shi]

Ma'anar Hadisin: "ya kasance idan yayi ruku'u yana rarraba Yatsunsa kuma idan yayi Sujada yana haxe Yatsunsa" ai cewa Manzon Allah SAW ya kasance idan ya kasance a Ruku'u yana kama Guiwoyinsa da Tafukan hannayensa kuma yana ya rarrabe tsakanin Yatsunsa; saboda wancan shi ne mafi cikiar ruku'u; kuma shi ne mafi tabbatar faruwar daidaita bayansa da Kansa, kuma amma a cikin Sujada sai ya sanya Tafukan Hannayensa a kan Qasa, kuma ya haxe yatsunsa ta yadda kowanne yana jikin xayan; don saboda ya samu cikar fuskantar Al-qibla da su, kuma shi ne mafi taimakawa kan jurewa a lokacin Sujada

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/10928